## SŪRATUḌ ḌUḤĀ سُورَةُ الضُّحَىٰ

Tana karantar da ni'imōmin da Allah Yã yi wa Annabi, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, a game da zãtinSa, dōmin Ya gina wasu hukunce-hukunce a kansu.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Inã rantsuwa da hantsi

*2.* Da dare a lõkacin da ya rufe (da duhunsa).

*3.* Ubangijinka bai yi maka bankwana ba, kuma bai ƙi ka ba.

*4.* Kuma lalle ta ƙarshe[1] ce mafi alheri a gare ka daga ta farko.

*5.* Kuma lalle ne Ubangijinka zai yi ta bã ka kyauta sai kã yarda.

*6.* Ashe, bai sãme ka marãya ba, sa'an nan Ya yi maka makõma?

*7.* Kuma Ya sãme ka bã ka da shari'ã, sai Ya shiryar da kai?

*8.* Kuma Ya sãme ka matalauci, sai Ya wadãtã ka?

*9.* Sabõda haka, amma marãya, to, kada ka rinjãye shi,

*10.* Kuma amma mai tambaya, kada ka yi masa tsãwa,

*11.* Kuma amma ni'imar Ubangijinka, sai ka faɗa (dõmin gõdiya)

وَٱلضُّحَىٰ ﴿١﴾

وَٱلَّيْلِ إِذَا سَجَىٰ ﴿٢﴾

مَا وَدَّعَكَ رَبُّكَ وَمَا قَلَىٰ ﴿٣﴾

وَلَلْءَاخِرَةُ خَيْرٌ لَّكَ مِنَ ٱلْأُولَىٰ ﴿٤﴾

وَلَسَوْفَ يُعْطِيكَ رَبُّكَ فَتَرْضَىٰٓ ﴿٥﴾

أَلَمْ يَجِدْكَ يَتِيمًا فَـَٔاوَىٰ ﴿٦﴾

وَوَجَدَكَ ضَآلًّا فَهَدَىٰ ﴿٧﴾

وَوَجَدَكَ عَآئِلًا فَأَغْنَىٰ ﴿٨﴾

فَأَمَّا ٱلْيَتِيمَ فَلَا تَقْهَرْ ﴿٩﴾

وَأَمَّا ٱلسَّآئِلَ فَلَا تَنْهَرْ ﴿١٠﴾

وَأَمَّا بِنِعْمَةِ رَبِّكَ فَحَدِّثْ ﴿١١﴾

(1) Ta ƙarshe, wãto, Lãhira; kuma ta farko, wato, dũniya.